Dakta Bukar Usman Dattijo Babban Mutum

Naja'atu Ta'annabi

Dr. Bukar Usman @80
10/12/2022

Naja'atu Ta'annabi



Dr. Bukar Usman @80
10/12/2022

Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Cafiya: Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Eyee, dattijo tsayayyen jigo turmin tsakar gida,
Cafiya: Datka Bukar Usman.
Rumfa sha shirgi uban gida ga masu gida,
Cafiya: Allahu ya dafa ma.
Dattijo Dakta Bukar Usman gada mahaɗa,
Cafiya: Dakta Bukar Usman
Jirgin sama kai ko babu ruwanka da gargada,
Cafiya: Allahu Ya dafa ma
Jajirtacce kake mai yin komai da ka'ida,
Cafiya: Dakta Bukar Usman

Mai taimakawa bayin Allah baya gudun gida.
Cafiya: Allah Ya dafa ma.
Tsohon ma'aikacin gwamnati mai kishin gida,
Cafiya:Dakta Bukar Usman
Mai taimakon marasa ƙarfi namu da fa'ida,
Cafiya:Allah Ya dafa ma.
Manoma yau sanadin ka suna ta hada-hada,
Cafiya:Dakta Bukar Usman.
Ka taimaka musu don bunƙasar ci gaban gida,
Cafiya: Allah Ya dafa ma.

Dakta Bukar Usmanu mun gaida gugan ƙarfe,
Sha gwagwarmaya ɗan baiwa,
Fagen alheri sada zumunci ka riga ka yi nisa,
Mai ƙarfin hali zuciyarka tsaye baka razana,

Ja gaba dai zaki ko a cikin dawa ka wuce bangaza,
Dakta Bukar Usman mu je, ka shiga duk sun fito waje
Naja'atu ce Ta'annabi ke maka waƙa jarumin gwagwarmaya,
Ga Addu'a gami da fatan khairi Allah ƙara lafiya.

Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Amshi: Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Eyee, ni da farko da sunan Wahidun Ahadun,
Mai dare Rabbi Mai rana Assamadun,
Har a kullum da Kai na dogara Majidun,
Gun ka dai ni nake bauta na Barradun,
Daɗa tsira salati gunsa Muhammadun,
Alihi har sahabu ban ga tamkarsu ba.

Amshi: Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Eyee, mai ƙashin arziki yau zan yi wa tambari,
Dakta Bukar Usman namu ne mai nazari,
Babban mutum mai karamci ne mai ƙoƙari,
Jarumi kake rana mai haske gari,
Haziƙin namiji barkanka da ƙoƙari,
Ka yi taka ka yi ta rago baka je ƙasa ba.

Amshi: Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Eyee, Dakta Bukar Usman shi dai dashen Rabbu ne,
Ka yi nisa tuni ka bar maza tsuggune,
Dakta Bukar Usman dama mashahuri ne,
Bare a yanzu kowa ya shaida kai wane ne.

Amshi: Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Eyee, ga fasihin mutum wanda duniya ke gani,
Dr Bukar Usman dattijo mai kwarjini,
Bajimin katibi marubuci ne gwani,
Mai littattafan da yake rabarwa gwani,
Jami'o'in ƙasa da wajen ƙasa sun gani,
Marubuci gwani duniya ba ta ƙi shi ba.

Amshi: Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba za ka tozarta ba.

Eyee, Dakta Bukar Usman namu kishi ne da shi,
Shugaban Ƙungiyar Manazarta ne fa shi,
A fagen adabi wani haziƙi ne fa shi,
A fagen tarihi wani littafi ne shi,
A fagen al'ada wata taska ce fa shi,
Marubuci Bukar dattijo ne shugaba.

Amshi: Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Eyee, mai zumunci da kyauta ba don a yabawa ba,
Komai zai yi don Allah ba don riya ba,
Alkhairi yake wani bai san ya yi ba,
Kuma baya buƙatar godiya nan gaba,
Naja Ta'annabi na shaida Dakta ya yi gaba,
Adali yake ya kafu ba zai faɗi ba.

Amshi: Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Eyee, ga mutum na mutane mai kyan zuciya,
Dakta Bukar Usman mai farar anniya,
Mai cikar nasaba mai wadatar zuciya,
Wanda abin sa baya rufe masa ido duniya,
Duka lamirinsa sauƙi ne ba fariya,
Haka yasa a kullum yake daɓa cigaba.

Amshi: Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Eyee, damuna kake ruwan sama ko ina ka zuba,
Mai samu ne da rabawa baka gaji ba,
Mai farin jinin jama’a waye bai sanka ba,
Ko ina an ji sunanka bai ɓuya ba,
Ka riga ka yi fice ba yau ba tun jiya,
Ka zamanto ruwan dare ko ina ka zuba.

Amshi: Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Eyee, magabata du'a'insu bai bar kanka ba,
Don kuwa ga shi kullum kana daɗin ci gaba,

Allahu ne Yai maka ba don iyawarka ba,
Ƙara gode Allah domin dadin ci gaba,
Allah Yasa ka ƙare lafiya Babban uba,
Ka cika da imani addu'a ba ma bar ta ba.

Amshi: Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Eyee, lafiya ka fara lafiya zaka gama,
Duka mai yi domin Allah zai girmama,
Addu'a ko da yaushe suke yima al'umma,
Rabbi Ya ja da kwana ka yi dadin sama,
Dakta Bukar Usman namu gaida kurtun zuma,
Makiyanka su yi haƙuri ba su ga karshenka ba.

Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

Amshi: Mai ƙashin arziki Allah Ya amince da kai,
Dakta Bukar Usman dattijo Babban mutum,
Gaskiya ka riƙe ba zaka tozarta ba.

_____

Naja'atu Ta'annabi mawakiya daga Kano ta kammala aikin rera wannan waƙa a sitidiyo a cikin Birnin Kano a ranar 16 ga watan Oktoba, 2024, Hakazalika Khalid Imam marubuci kuma malamin makaranta a Birnin Kano ya rubuta cikin matanin da za a iya karantawa ko nazari a ranar 18 ga watan Oktoba, 2024. Wannan waƙa Khalid Imam ya juya matanin a cikin Turanci a ranar 24 ga watan Nuwamba, 2024.

Dr. Bukar Usman the Honourable Elder Statesman

Naja'atu Ta'annabi

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always
Your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

Verse: Yee, the steadfast elder statesman, the community centre-piece,
Interjection: Dr. Bukar Usman
Verse: O friendly canopy a strong pillar to many
Interjection: May Allah assist you
Verse: Elder Dr. Bukar Usman, O connecting bridge
Interjection: Dr. Bukar Usman
Verse: Like the plane, seamlessly you travail, bump-less
Interjection: May Allah assist you
Verse: Law-abiding hard worker that you are
Interjection: Dr. Bukar Usman

Verse: Magnanimous non-prodigal helper you are
Interjection: May Allah assist you,
Verse: Patriotic and astute retired civil servant,
Interjection: Dr. Bukar Usman
Verse: O kind tender of the weak and struggling,
Interjection: May Allah assist you
Verse: Farmers are up and doing with your aid
Interjection: Dr. Bukar Usman
Verse: Handy hoe in the nation's agricultural flourish
Interjection: May Allah assist you

Verse: May Allah assist you, Dr. Bukar Usman, sturdy vessel that you are
Interjection: We hail you,
O blessed striving soul
Unrivaled you are in kindness and cordiality
O courageous strong-hearted Knight, solid as a rock
Go ahead, Lion, in the forests, you're beyond scare
Dr. Bukar Usman, lead the way,
You forged ahead when they backed off
It's Naja'atu Ta'annabi singing your praises, O hero of struggles,
A prayer and a plea – may Allah increase your wellbeing.

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always, your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

Verse: I begin my praise in the name of the Almighty, The One and Only Controller of days and nights, the Eternal Absolute
You are my Anchor, O Most Honorable
My worship is solely for You –
Shower peace and blessings upon Muhammad,
His progeny and companions; their likes I have not seen.

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always, your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

Verse: Today the naturally-endowed I shall hail
Dr. Bukar Usman, the scholarly researcher
Great, admirable generous man who strives…
O brave, you are a bright shining star,
O assiduous man, all praise your efforts,
You conquered all, firm without falling.

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always, your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

Verse: Dr. Bukar Usman, a sapling planted by God,
Ahead you've marched, leaving others squatting,
Dr. Bukar Usman, already famed you are;
Today, the world knows your worth,
May your end be great, o heroic elder,
Dr. Bukar Usman, Allah-conscious you are.

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always, your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

Verse: Behold! You are famed across the world,
Dr. Bukar Usman, the charismatic elder –
Great author, with literary expertise,
Distributing his works magnanimously for free
Your books are studied in universities globally,
A famed writer accepted by the world.

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always, your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

Verse: Our Dr. Bukar Usman patriotic is he,
A leader to Literary Critics and Researchers,
In the field of Literature a genius he is,

An Encyclopedia in the field of history
And Treasure Chest in the cultural realm…
Writer Bukar is indeed an elder and leader.

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always, your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

Verse: Yee, here's a caring kinsman, a benevolent soul,
With a pure heart and gifting hands requiring no thanks,
Sharing goodness for the sake of God,
A man with a noble lineage and a content heart,
Simple in his affairs, not prone to bragging,
I, Naja Ta'Annabi, a witness to the progress
Of this just, equitable, un-crumbling Pillar!

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always, your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

Here's one loved by all, the pure-hearted,
Dr. Bukar Usman, the well-meaning
Noble Soul with a content Heart
Whose possessions never blindfold him
Humble in his affairs, never found bragging,
Hence his generosity a ladder to his progress!

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always, your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

Verse: A rainy season, showering raindrops everywhere –
He who acquires and shares without tiring,
Adorable to the people, who's unaware of you?
Your name has spread everywhere,
Outstanding you are yesterday and today,
A night downpour, present everywhere.

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always, your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

Verse: Yee, the prayers of thy ancestors haven't left thee,
Your rapid progress, a living testimony
Blessed by Allah you are, not just your doings
Praise Him the more, for greater progress
May you end well, o great father,

With faith on your lips, we pray.

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always, your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

Verse: You started well and so shall you end well,
All who do good for Allah's sake shall soar,
Prayed for by all and sundry,
May Allah prolong and uplift your life.
O, Dr. Bukar Usman! We greet our honeypot,
You've outshined your foes, O full moon!

Chorus: *O fortunate rich, God has accepted you,*
Dr. Bukar Usman the honourable elder statesman,
You upheld the truth always, your end shall be a great fortune
Interjection: You upheld the truth always, your end shall be a great fortune

_____

Naja'atu Ta'Annabi a song artist from Kano rendered this song initially in Hausa in Kano on 16th October, 2024. Khalid Imam a poet, education administrator and a freelance researcher also based in Kano, transcribed the song on 18th October, 2024, and translated it into English in a readable and analyzable format on 24th November, 2024.